An tambayi Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi - game da mafi yawan abin da yake shigar da mutane aljanna, sai ya ce: "Tsoron Allah da kyawawan ɗabi'u

Daga Abu Huraira - Allah Ya yarda da shi - ya ce: An tambayi Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi - game da mafi yawan abin da yake shigar da mutane aljanna, sai ya ce: "Tsoron Allah da kyawawan ɗabi'u", kuma an tambayeshi game da mafi yawan abin da yake shigar da mutane wuta sai ya ce: "Baki da farji".
[Hasan ne kuma Ingantacce] [Tirmizi da Ibnu Majah da Ahmad Suka ruwaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a greshi - yana bayyana cewa mafi giman sababban da suke shigar da mutane aljanna sababba biyu ne, sune: Tsoron Allah da kyawawan ɗabi'u. Tsoron Allah: Shi ne ka sanya kariya tsakaninka da tsakanin azabar Allah, ta hanyar aikata umarninsa da nisantar hane-hanensa. Kyakkyawar ɗabi'a: Tana kasancewa ne da shinfiɗar fuska, da yin aikin kirki, da kamewa daga cuta. Kuma mafi girman sababban da suke shigarwa wuta sababba biyu ne, su ne: Harshe da farji. yana daga saɓon harshe: Ƙarya, da raɗa, da annamimanci da wasunsu. Yana daga saɓon farji: Zina da luwaɗi da wasunsu.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/5476